جمعية الدعوة والتعليم باللغات الأفريقية
Da'wah and Education in African Languages

# دور المرأة المسلمِة في بناء الأسرة الصالحة

# Matsayin Mace Musulma wajen Gina Iyali Nagari

## الْمُقدِمَةُ

الْحَمْدُ لِلَّهِ رَبِّ الْعَالَمِينَ، وَالصَّلَاةُ وَالسَّلَامُ عَلَى نَبِيِّنَا مُحَمَّدٍ، وَعَلَى آلِهِ وَصَحْبِهِ أَجْمَعِينَ.

Godiya ta tabbata ga Allah, Ubangijin talikai

Tsira da amincin Allah su tabbata ga Annabinmu Muhammadu, da iyalansa da sahabbansa baki ɗaya

إِنَّ الْأُسْرَةَ فِي الْإِسْلَامِ لَيْسَتْ مُجَرَّدَ بَيْتٍ يَجْتَمِعُ فِيهِ الزَّوْجُ وَالزَّوْجَةُ وَالْأَبْنَاءُ، وَإِنَّمَا هِيَ مَدْرَسَةُ الْإِيمَانِ وَالْأَخْلَاقِ، وَمَهْدُ الْأَجْيَالِ، وَأَسَاسُ الْمُجْتَمَعِ الصَّالِحِ.

Iyali a Musulunci ba kawai gida ba ne inda miji da mata da 'ya'ya suke taruwa

A'a, iyali makarantar imani da kyawawan ɗabi'u ce,kuma shimfiɗar da ake gina al'ummai a kanta ce.

Haka kuma iyali ita ce ginshikin al'umma ta gari.

وَإِذَا صَلَحَتِ الْأُسْرَةُ صَلَحَ الْمُجْتَمَعُ، وَإِذَا اضْطَرَبَتِ الْأُسْرَةُ انْعَكَسَ اضْطِرَابُهَا عَلَى الْأَبْنَاءِ وَالْمُجْتَمَعِ كُلِّهِ.

Idan iyali suka gyaru, al'umma ma za ta gyaru.Idan kuma iyali suka lalace ko suka rikice,

rikicinsu zai shafi 'ya'ya da kuma al'umma baki ɗaya.

وَالْمَرْأَةُ الْمُسْلِمَةُ لَهَا دَوْرٌ عَظِيمٌ فِي بِنَاءِ هَذِهِ الْأُسْرَةِ؛ فَهِيَ زَوْجَةٌ وَأُمٌّ وَمُرَبِّيَةٌ، وَقَدْ تَكُونُ كَذَلِكَ مَصْدَرًا لِلسَّكِينَةِ وَالْحِكْمَةِ وَالْإِيمَانِ دَاخِلَ بَيْتِهَا.

Mace Musulma tana da babban matsayi wajen gina wannaniyali.

Ita mata ce,

kuma uwa ce,

kuma mai tarbiyya ce.

Haka kuma tana iya kasancewa tushen natsuwa,

da hikima,

da imani a cikin gidanta.

وَهَذَا الدَّوْرُ لَا يَعْنِي أَنَّ مَسْؤُولِيَّةَ الْأُسْرَةِ تَقَعُ عَلَى الْمَرْأَةِ وَحْدَهَا، فَالْإِسْلَامُ حَمَّلَ الرَّجُلَ وَالْمَرْأَةَ مَسْؤُولِيَّاتٍ مُتَكَامِلَةً.

Wannan matsayi ba yana nufin cewa nauyin kula da iyali yanakan mace ita kaɗai ba.

Musulunci ya ɗora wa namiji da mace nauyuka daban-dabanwaɗanda suke taimakon juna.

Abin da ake nufi shi ne bayyana irin babban matsayi da
Musulunci ya bai wa mace,
wajen gyara gidanta,
da kuma tarbiyyar 'ya'yanta.

وَمِنْ هُنَا تَأْتِي هَذِهِ الرِّسَالَةُ إِلَى الْمَرْأَةِ الْمُسْلِمَةِ فِي إِفْرِيقِيَا.

Daga nan ne wannan sako yake zuwa ga mace Musulma a Afirka.

الْمَرْأَةِ الَّتِي تَجْمَعُ بَيْنَ اعْتِزَازِهَا بِدِينِهَا، وَارْتِبَاطِهَا بِأُسْرَتِهَا وَمُجْتَمَعِهَا، وَحِرْصِهَا عَلَى مُسْتَقْبَلِ أَبْنَائِهَا.

Mace wadda take alfahari da addininta,
kuma take da alaƙa mai ƙarfi da iyalinta da al'ummarta,
kuma take kula da makomar 'ya'yanta.

لِتَقُولَ لَهَا: إِنَّ بِنَاءَ الْأُمَّةِ يَبْدَأُ مِنِ اسْتِقْرَارِ الْبَيْتِ.

Domin a ce mata:
Gina al'umma yana farawa ne daga kwanciyar hankalin gida.

وَإِنَّ أَعْظَمَ مَا تَسْتَطِيعِينَ أَنْ تُقَدِّمِيهِ لِأُمَّتِكِ أَنْ تَبْنِي جِيلًا مُؤْمِنًا، صَالِحًا، مُعْتَزًّا بِدِينِهِ وَهُوِيَّتِهِ، نَافِعًا لِأَهْلِهِ وَمُجْتَمَعِهِ.

Kuma babban abin da za ki iya ba wa al'ummarki shi ne,
ki gina tsararriyar ƙarni mai imani da nagarta,
mai alfahari da addininsa da asalinsa,
mai amfani ga iyalinsa da al'ummarsa.

## أَوَّلًا: الْأُسْرَةُ الصَّالِحَةُ مَسْؤُولِيَّةٌ مُشْتَرَكَةٌ

## .Na farko: Iyali na gari nauyi ne na kowa

يَبَّنَ الْقُرْآنُ الْكَرِيمُ أَنَّ حِمَايَةَ الْأُسْرَةِ مِنَ الِانْحِرَافِ مَسْؤُولِيَّةٌ عَظِيمَةٌ.

Alƙur'ani Mai Girma ya bayyana cewa,

.kare iyali daga karkacewa da lalacewa babban nauyi ne

قَالَ اللهُ تَعَالَى:

Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا قُوا أَنْفُسَكُمْ وَأَهْلِيكُمْ نَارًا﴾

"Ya ku waɗanda suka yi imani!
Ku kare kanku da iyalanku daga Wuta."

فَالْآيَةُ تُوَجِّهُ الْمُؤْمِنَ إِلَى الْعِنَايَةِ بِنَفْسِهِ وَأَهْلِهِ.

Wannan aya tana shiryar da mumini zuwa ga kula da kansa da iyalinsa.

وَمِنْ صُوَرِ ذَلِكَ تَعْلِيمُهُمُ الْخَيْرَ، وَتَرْبِيَتُهُمْ عَلَى الطَّاعَةِ، وَتَحْذِيرُهُمْ مِنْ أَسْبَابِ الِانْحِرَافِ.

Daga cikin hakan akwai:
,a koya musu alheri
,a tarbiyantar da su a kan biyayya
.a kuma gargaɗe su daga abubuwan da suke jawo karkacewa

وَقَدْ ذَكَرَ الْمُفَسِّرُونَ أَنَّ مِنْ مَعَانِي الْآيَةِ تَعْلِيمَ الْأَهْلِ وَتَأْدِيبَهُمْ، وَأَمْرَهُمْ

بِالْخَيْرِ، وَنَهْيَهُمْ عَنِ الشَّرِّ.

Masu tafsiri sun bayyana cewa daga cikin ma'anar
wannan ayaakwai:
koyar da iyali,
tarbiyantar da su,
umartar su da alheri,
da kuma hana su aikata sharri.

وَهُنَا تُدْرِكُ الْمَرْأَةُ الْمُسْلِمَةُ أَنَّ تَرْبِيَتَهَا لِأَبْنَائِهَا لَيْسَتْ عَمَلًا هَامِشِيًّا، بَلْ هِيَ

عِبَادَةٌ وَمَسْؤُولِيَّةٌ وَأَمَانَةٌ.

A nan mace Musulma za ta fahimci cewa,
tarbiyyar da take yi wa 'ya'yanta ba wani ƙaramin aiki ba ne.
A'a, ibada ce, kuma nauyi ne, kuma amana ce.

الطِّفْلُ الَّذِي يَنْشَأُ فِي بَيْتٍ يَتَعَلَّمُ فِيهِ الصَّلَاةَ وَالصِّدْقَ وَالرَّحْمَةَ وَاحْتِرَامَ الْوَالِدَيْنِ، يَحْمِلُ هَذِهِ الْقِيَمَ مَعَهُ عِنْدَمَا يَكْبَرُ.

Yaron da ya girma a gidan da ake koya masa sallah, da
gaskiya,da tausayi, da girmama iyaye, zai tafi da waɗannan
kyawawanhalaye tare da shi yayin da ya girma.

وَقَدْ يُصْبِحُ بِهَا سَبَبًا فِي إِصْلَاحِ مُجْتَمَعِهِ.

Kuma wata rana zai iya zama sanadin gyaran al'ummarsa.

# ثَانِيًا: الْمَرْأَةُ رَاعِيَةٌ فِي بَيْتِهَا

## .Na biyu: Mace mai kula ce a gidanta

قَالَ رَسُولُ اللهِ ﷺ:

:ya ce ﷺ Manzon Allah

«كُلُّكُمْ رَاعٍ، وَكُلُّكُمْ مَسْئُولٌ عَنْ رَعِيَّتِهِ... وَالْمَرْأَةُ رَاعِيَةٌ عَلَى بَيْتِ
زَوْجِهَا وولَدِهِ، فَكُلُّكُمْ رَاعٍ وكُلُّكُمْ مَسْئُولٌ عَنْ رَعِيَّتِهِ».

"Kowannenku makiyayi ne, kuma kowannenku za a tambaye shigame da abin da yake kula da shi. Mace kuma mai kula ce da gidan mijinta da 'ya'yansa.
Saboda haka kowannenku makiyayi ne,
kuma kowannenku za a tambaye shi game da abin da yake kula da shi."

وَهُوَ حَدِيثٌ صَحِيحٌ مُتَّفَقٌ عَلَيْهِ.

Wannan hadisi ne ingantacce,
wanda Bukhari da Muslim suka ruwaito.

وَهَذَا الْحَدِيثُ يَمْنَحُ الْمَرْأَةَ الْمُسْلِمَةَ تَصَوُّرًا وَاضِحًا عَنْ مَكَانَتِهَا وَمَسْؤُولِيَّتِهَا.

Wannan hadisi yana ba mace Musulma cikakken fahimta game da matsayinta da nauyinta.

فَهِيَ لَيْسَتْ مُجَرَّدَ فَرْدٍ يَعِيشُ دَاخِلَ الْأُسْرَةِ، وَإِنَّمَا هِيَ رَاعِيَةٌ مَسْؤُولَةٌ عَنْ جَانِبٍ مُهِمٍّ مِنْ جَوَانِبِهَا.

Ba kawai mutum ce da take rayuwa a cikin iyali ba. A'a, ita maikula ce,
kuma tana da alhakin wani muhimmin ɓangare na iyalin.

وَالرِّعَايَةُ لَا تَعْنِي الْقِيَامَ بِالْأَعْمَالِ الْمَنْزِلِيَّةِ فَقَطْ، وَإِنَّمَا تَشْمَلُ الرِّعَايَةَ النَّفْسِيَّةَ وَالتَّرْبَوِيَّةَ وَالْإِيمَانِيَّةَ وَالْأَخْلَاقِيَّةَ.

Kulawa ba yana nufin ayyukan gida kawai ba. A'a, ta ƙunshi:kulawa da yanayin zuciya da tunanin 'ya'ya, da tarbiyya, da imani, da kuma kyawawan ɗabi'u.

فَالْأُمُّ الَّتِي تَسْتَمِعُ لِأَبْنَائِهَا، وَتُعَلِّمُهُمُ الصَّلَاةَ، وَتُرَبِّيهِمْ عَلَى الصِّدْقِ، وَتَغْرِسُ فِيهِمْ احْتِرَامَ الْآخَرِينَ، وَتُرَاقِبُ مَا يُشَاهِدُونَهُ وَمَا يَتَعَلَّمُونَهُ، تُمَارِسُ دَوْرًا أَسَاسِيًّا فِي صِنَاعَةِ مُسْتَقْبَلِ الْأُسْرَةِ.

Uwar da take sauraron 'ya'yanta, kuma take koya musu sallah,kuma take tarbiyantar da su a kan gaskiya, kuma take dasa musugirmama sauran mutane,
kuma take kula da abubuwan da suke kallo da abubuwan da suke koya,
tana taka muhimmiyar rawa wajen gina makomar iyali.

# ثَالِثًا: الْمَرْأَةُ الصَّالِحَةُ مَصْدَرٌ لِلسَّكِينَةِ وَالْمَوَدَّةِ

## .Na uku: Mace ta gari tushen natsuwa da ƙauna ce

مِنْ أَعْظَمِ مَقَاصِدِ الزَّوَاجِ فِي الْإِسْلَامِ أَنْ يَكُونَ الْبَيْتُ مَكَانًا لِلسَّكِينَةِ وَالْمَوَدَّةِ وَالرَّحْمَةِ.

**Daga cikin manyan manufofin aure a Musulunci akwai, gida yazama wurin natsuwa, da ƙauna, da rahama.**

قَالَ اللهُ تَعَالَى

**Allah Maɗaukaki Ya ce:**

﴿وَمِنْ آيَاتِهِ أَنْ خَلَقَ لَكُمْ مِنْ أَنْفُسِكُمْ أَزْوَاجًا لِتَسْكُنُوا إِلَيْهَا وَجَعَلَ بَيْنَكُمْ مَوَدَّةً وَرَحْمَةً﴾

**"Daga cikin ayoyinSa akwai Ya halitta muku matan aure dagacikinku, domin ku sami natsuwa a wurinsu, kuma Ya sanyasoyayya da rahama a tsakaninku."**

فَالْأُسْرَةُ الصَّالِحَةُ لَا تَقُومُ عَلَى الْمَالِ وَحْدَهُ، وَلَا عَلَى الْمَسْكَنِ الْجَمِيلِ، وَلَا عَلَى كَثْرَةِ الْأَبْنَاءِ،
وَإِنَّمَا تَقُومُ قَبْلَ ذَلِكَ عَلَى الْإِيمَانِ وَالْمَوَدَّةِ وَالرَّحْمَةِ وَحُسْنِ التَّعَامُلِ.

**Iyali na gari ba ya ginuwa da kuɗi kaɗai. Ba ya ginuwa da kyakkyawan gida kawai. Ba ya ginuwa da yawan 'ya'ya kawai. Maimakon haka, kafinkomai, yana ginuwa ne a kan imani, da ƙauna, da rahama, da kyakkyawar mu'amala.**

وَالْمَرْأَةُ تَسْتَطِيعُ أَنْ تُسْهِمَ فِي صِنَاعَةِ هَذَا الْجَوِّ مِنْ خِلَالِ حُسْنِ الْكَلَامِ، وَاحْتِرَامِ الزَّوْجِ، وَالصَّبْرِ عِنْدَ الْخِلَافِ، وَتَجَنُّبِ إِهَانَةِ أَفْرَادِ الْأُسْرَةِ، وَالْحِرْصِ عَلَى أَنْ يَكُونَ الْبَيْتُ مَكَانًا يَجِدُ فِيهِ الزَّوْجُ وَالْأَبْنَاءُ الْأَمَانَ وَالطُّمَأْنِينَةَ.

**Mace za ta iya taimakawa wajen samar da irin wannan yanayi, ta hanyar kyakkyawar magana, da girmama miji, da haƙuri lokacinsaɓani, da guje wa wulaƙanta wani daga cikin iyali, da kumaƙoƙarin ganin cewa gida ya zama wurin da miji da 'ya'ya sukesamun aminci da kwanciyar hankali.**

وَفِي الْمُقَابِلِ، فَإِنَّ هَذَا وَاجِبٌ مُشْتَرَكٌ بَيْنَ الزَّوْجَيْنِ؛ فَكَمَا أَنَّ الْمَرْأَةَ مُطَالَبَةٌ بِحُسْنِ الْمُعَاشَرَةِ، فَإِنَّ الرَّجُلَ مَأْمُورٌ كَذَلِكَ بِحُسْنِ مُعَامَلَةِ زَوْجَتِهِ وَأُسْرَتِهِ.

**A gefe guda kuma, wannan nauyi ne na ma'aurata duka. Kamar yadda ake buƙatar mace ta kyautata mu'amala da mijinta, haka ma namiji an umarce shi da ya kyautata mu'amala da matarsa da iyalinsa.**

# رَابِعًا: تَرْبِيَةُ الْأَبْنَاءِ عَلَى الْعَقِيدَةِ وَالْعِبَادَةِ

## .Na huɗu: Tarbiyyar 'ya'ya a kan aqida da ibada

أَعْظَمُ مَا يُمْكِنُ أَنْ تُقَدِّمَهُ الْأُمُّ لِأَبْنَائِهَا هُوَ أَنْ تَرْبِطَ قُلُوبَهُمْ بِاللهِ تَعَالَى.

Babban abin da uwa za ta iya ba wa 'ya'yanta shi ne, ta haɗazukatansu da Allah Maɗaukaki.

قَالَ اللهُ تَعَالَى:

Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَأْمُرْ أَهْلَكَ بِالصَّلَاةِ وَاصْطَبِرْ عَلَيْهَا﴾

"Ka umarci iyalinka da yin sallah, kuma ka yi hakuri a kanta."

فَالصَّلَاةُ لَيْسَتْ عَادَةً يُؤَدِّيهَا الطِّفْلُ دُونَ فَهْمٍ، وَإِنَّمَا هِيَ صِلَةٌ بَيْنَ الْعَبْدِ وَرَبِّهِ.

Sallah ba wata al'ada ce da yaro yake yi ba tare da fahimta ba.A'a, sallah alaƙa ce tsakanin bawa da Ubangijinsa.

وَلِذَلِكَ يَنْبَغِي لِلْأُمِّ أَنْ تُعَوِّدَ أَبْنَاءَهَا عَلَيْهَا مُنْذُ الصِّغَرِ، وَأَنْ تَجْعَلَ الْعِبَادَةَ مُرْتَبِطَةً بِالْحُبِّ وَالْإِيمَانِ، لَا بِالْخَوْفِ وَالْعُقُوبَةِ وَحْدَهُمَا.

Saboda haka ya kamata uwa ta saba da 'ya'yanta da yin sallahtun suna ƙanana. Kuma ta sanya ibada ta kasance tare da ƙauna da imani, ba tsoro da hukunci kaɗai ba.

كَمَا يَنْبَغِي أَنْ تَحْرِصَ الْمَرْأَةُ عَلَى تَعْلِيمِ أَبْنَائِهَا الْقُرْآنَ الْكَرِيمَ، وَالْأَذْكَارَ، وَالسِّيرَةَ النَّبَوِيَّةَ، وَالْأَخْلَاقَ الْإِسْلَامِيَّةَ، مَعَ تَقْدِيمِ الْقُدْوَةِ الْعَمَلِيَّةِ لَهُمْ.

Haka kuma ya kamata mace ta kula da koyar da 'ya'yantaAlkur'ani Mai Girma, da addu'o'i da zikiri, da tarihin rayuwar Annabi ﷺ, da kyawawan ɗabi'un Musulunci.Tare da kasancewa abin koyi a aikace a gare su.

فَالطِّفْلُ يَتَعَلَّمُ مِمَّا يَرَاهُ فِي الْبَيْتِ أَكْثَرَ مِمَّا يَتَعَلَّمُ مِنَ الْكَلِمَاتِ.

Yaro yana koyon abin da yake gani a gida, fiye da abin da yakekoya daga kalmomi kawai.

إِذَا رَأَى الِابْنُ أُمَّهُ تُحَافِظُ عَلَى الصَّلَاةِ، وَتَصْدُقُ فِي كَلَامِهَا، وَتَحْتَرِمُ وَالِدَيْهَا، وَتُسَاعِدُ الْمُحْتَاجَ، وَتَضْبِطُ غَضَبَهَا، فَإِنَّهُ يَتَعَلَّمُ الْإِسْلَامَ مِنْ وَاقِعِ الْحَيَاةِ.

Idan ɗa ya ga mahaifiyarsa tana kiyaye sallah, kuma tana faɗingaskiya, kuma tana girmama iyayenta, kuma tana taimaka wa mabukata,kuma tana sarrafa fushinta, to zai koyi Musulunci daga rayuwarzahiri.

## خَامِسًا: الْمَرْأَةُ الْإِفْرِيقِيَّةُ وَدَوْرُهَا فِي الْمُحَافَظَةِ عَلَى الْهُوِيَّةِ الْإِسْلَامِيَّةِ

## Na biyar: Matar Afirka da rawar da take takawa wajen .kiyayeasalin Musulunci

أَيَّتُهَا الْأُخْتُ الْمُسْلِمَةُ فِي إِفْرِيقِيَا، إِنَّكِ تَعِيشِينَ فِي بِيئَاتٍ مُتَنَوِّعَةٍ، تَخْتَلِفُ فِيهَا اللُّغَاتُ وَالثَّقَافَاتُ وَالْعَادَاتُ وَالتَّقَالِيدُ.

Y a ke 'yar'uwa Musulma a Afirka, kina rayuwa ne a cikinwurare daban-daban,
.inda harsuna, al'adu, ɗabi'u da al'adun gargajiya suke bambanta

وَهَذِهِ الثَّرْوَةُ الثَّقَافِيَّةُ لَيْسَتْ بِالضَّرُورَةِ عَائِقًا أَمَامَ الْإِسْلَامِ.

.Wannan arzikin al'adu ba lallai ne ya zama cikas ga Musulunciba

فَالْإِسْلَامُ جَاءَ لِيُهَذِّبَ الْعَادَاتِ الْمُخَالِفَةَ لِلشَّرْعِ، وَيُحَافِظَ عَلَى مَا كَانَ مِنْهَا صَالِحًا.

,Musulunci ya zo ne domin ya gyara al'adun da suka saɓa washari'a
.kuma ya kiyaye waɗanda suke da kyau da amfani

وَمِنْ هُنَا فَإِنَّ مَسْؤُولِيَّتَكِ لَيْسَتْ أَنْ تَتَخَلَّي عَنْ ثَقَافَتِكِ الْإِفْرِيقِيَّةِ، وَإِنَّمَا أَنْ تُمَيِّزِي بَيْنَ مَا هُوَ مِنَ الْعَادَاتِ النَّافِعَةِ وَمَا يُخَالِفُ عَقِيدَةَ الْإِسْلَامِ وَأَخْلَاقَهُ وَأَحْكَامَهُ.

.Saboda haka, nauyinki ba wai ki bar al'adunki na Afirka ba ne
,A'a, abin da ake bukata shi ne ki bambanta tsakanin: al'adun da suke da amfani
,da kuma abubuwan da suka saɓa wa aqidar Musulunci, da ɗabi'unsa
.da hukunce-hukuncensa

عَلِّمِي أَبْنَاءَكِ أَنْ يَكُونُوا مُسْلِمِينَ مُعْتَزِّينَ بِدِينِهِمْ، وَفِي الْوَقْتِ نَفْسِهِ مُحِبِّينَ لِأَوْطَانِهِمْ وَمُجْتَمَعَاتِهِمْ، مُحْتَرِمِينَ لِلنَّاسِ، مُتَعَاوِنِينَ مَعَهُمْ فِي الْخَيْرِ.

Ki koya wa 'ya'yanki su kasance Musulmai masu alfahari da addininsu. A lokaci guda kuma, su kasance masu son ,ƙasashensuda al'ummominsu, masu girmama kuma masu taimaka musu wajen ayyukan alheri.mutane

قَالَ اللهُ تَعَالَى:

Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿إِنَّ أَكْرَمَكُمْ عِنْدَ اللهِ أَتْقَاكُمْ﴾

"Lallai mafi darajarku a wurin Allah shi ne wanda ya fi kutaƙawa."

فَلَا يَنْبَغِي أَنْ يَشْعُرَ الْمُسْلِمُ الْإِفْرِيقِيُّ أَنَّ إِسْلَامَهُ يَتَعَارَضُ مَعَ هُوِيَّتِهِ الْإِفْرِيقِيَّةِ.

Bai kamata Musulmin Afirka ya ji cewa Musuluncinsa yanakaro da asalin Afirkansa ba.

بَلْ يُمْكِنُهُ أَنْ يَجْمَعَ بَيْنَ الِاعْتِزَازِ بِدِينِهِ، وَخِدْمَةِ مُجْتَمَعِهِ، وَالْمُحَافَظَةِ عَلَى مَا فِي ثَقَافَتِهِ مِنْ قِيَمٍ حَسَنَةٍ.

A'a, zai iya haɗa tsakanin: alfahari da addininsa, da hidima ga da kuma kiyaye kyawawan ƙimomin da suke
,cikin al'adunsa.al'ummarsa

# سَادِسًا: الْأُمُّ الْمُسْلِمَةُ قُدْوَةٌ قَبْلَ أَنْ تَكُونَ مُرَبِّيَةً

## Na shida: Uwar Musulma abin koyi ce kafin ta zama .maitarbiyya

مِنَ الْأَخْطَاءِ الَّتِي قَدْ تَقَعُ فِيهَا بَعْضُ الْأُمَّهَاتِ أَنْ تُكْثِرَ مِنْ تَقْدِيمِ النَّصَائِحِ لِأَبْنَائِهَا دُونَ أَنْ تُقَدِّمَ لَهُمْ نَمُوذَجًا عَمَلِيًّا.

,Daga cikin kura-kuran da wasu iyaye mata za su iya faɗawaakwai

.yawan ba ’ya’yansu nasiha, ba tare da ba su kyakkyawan misalina aikace ba

فَكَيْفَ نَطْلُبُ مِنَ الِابْنَةِ الصِّدْقَ وَأُمُّهَا تَكْذِبُ؟

,Ta yaya za mu nemi ’ya mace ta kasance mai gaskiya

?alhali mahaifiyarta tana yin ƙarya

وَكَيْفَ نَطْلُبُ مِنَ الِابْنِ احْتِرَامَ الْآخَرِينَ وَهُوَ يَرَى وَالِدَيْهِ يَتَشَاجَرَانِ أَمَامَهُ؟

,Ta yaya za mu nemi ɗa ya girmama mutane

?alhali yana ganin iyayensa suna rigima a gabansa

وَكَيْفَ نَطْلُبُ مِنَ الِابْنِ احْتِرَامَ الْآخَرِينَ وَهُوَ يَرَى وَالِدَيْهِ يَتَشَاجَرَانِ أَمَامَهُ؟

,Ta yaya za mu nemi ɗa ya girmama mutane

?alhali yana ganin iyayensa suna rigima a gabansa

وَكَيْفَ نُطَالِبُهُ بِالْمُحَافَظَةِ عَلَى الصَّلَاةِ إِذَا كَانَتِ الصَّلَاةُ فِي الْبَيْتِ أَمْرًا ثَانَوِيًّا؟

?Ta yaya za mu nemi ya kiyaye sallah, idan ana ɗaukar sallah a gida a matsayin abu na biyu

إِنَّ التَّرْبِيَةَ بِالْقُدْوَةِ مِنْ أَقْوَى وَسَائِلِ التَّأْثِيرِ.

.Tarbiyya ta hanyar kyakkyawan misali tana daga cikin hanyoyinda suka fi ƙarfi wajen tasiri

وَالْمَرْأَةُ الَّتِي تُرِيدُ أُسْرَةً صَالِحَةً يَنْبَغِي أَنْ تَبْدَأَ بِإِصْلَاحِ نَفْسِهَا.

Matar da take son samun iyali na ga ya kamata ta fara da gyarakanta.ri

فَتَتَعَلَّمُ دِينَهَا، وَتُحَافِظُ عَلَى عِبَادَتِهَا، وَتَتَحَلَّى بِالصَّبْرِ، وَتُرَاقِبُ لِسَانَهَا، وَتُحْسِنُ تَعَامُلَهَا مَعَ زَوْجِهَا وَأَبْنَائِهَا وَجِيرَانِهَا وَأَقَارِبِهَا.

,Ta koyi addininta, ta kiyaye ibadarta, ta kasance mai haƙuri

ta kula da harshenta, kuma ta kyautata mu’amalarta da mijinta,da ’ya’yanta, da maƙwabtanta, da kuma ’yan .uwanta

فَالْبَيْتُ الَّذِي تُوجَدُ فِيهِ أُمٌّ صَالِحَةٌ لَا يَعْنِي بَيْتًا بِلَا مُشْكِلَاتٍ.

Gidan da yake da uwa ta gari ba yana nufin gida ne da babu matsaloli ba.

وَإِنَّمَا يَعْنِي بَيْتًا يَعْرِفُ أَهْلُهُ كَيْفَ يُعَالِجُونَ الْمُشْكِلَاتِ بِالْإِيمَانِ وَالْحِكْمَةِ وَالرَّحْمَةِ.

A’a, yana nufin gida ne wanda mutanensa suka san yadda za sumagance matsaloli, da imani, da hikima, da rahama.

## سَابِعًا: الْحِوَارُ وَالْحُبُّ فِي تَرْبِيَةِ الْأَبْنَاءِ

## .Na bakwai: Hira da ƙauna wajen tarbiyyar 'ya'ya

تَحْتَاجُ الْأُسْرَةُ الْمُسْلِمَةُ الْيَوْمَ إِلَى الْحِوَارِ أَكْثَرَ مِنْ أَيِّ وَقْتٍ مَضَى.

Iyali Musulmi a yau suna bukatar tattaunawa fiye da kowanelokaci.

فَالْأَبْنَاءُ يَتَعَرَّضُونَ لِمُؤَثِّرَاتٍ كَثِيرَةٍ مِنَ الْهَاتِفِ وَالْإِنْتَرْنِتِ وَوَسَائِلِ التَّوَاصُلِ الِاجْتِمَاعِيِّ وَالْأَصْدِقَاءِ وَالْمَدْرَسَةِ وَالْمُجْتَمَعِ.

,Ya'ya suna fuskantar tasiri iri-iri, daga wayar hannu da intanet'

.da kafafen sada zumunta, da abokai, da makaranta, da kumaal'umma

وَلِهَذَا لَا يَكْفِي أَنْ تَقُولَ الْأُمُّ لِابْنِهَا: «هَذَا حَرَامٌ» أَوْ «لَا تَفْعَلْ ذَلِكَ».

:Saboda haka, bai isa uwa ta ce wa ɗanta kawai: "Wannanharamun ne," ko kuma

".Kada ka yi haka"

بَلْ يَنْبَغِي أَنْ تَشْرَحَ لَهُ لِمَاذَا، وَأَنْ تَسْمَعَ مِنْهُ، وَأَنْ تَجْعَلَهُ يَشْعُرُ

بِأَنَّهُ يَسْتَطِيعُ الرُّجُوعَ إِلَيْهَا عِنْدَمَا يُوَاجِهُ مُشْكِلَةً.

,A'a, ya kamata ta bayyana masa dalilin hakan, ta saurare shi

kuma ta sa shi ya ji cewa zai iya komawa wurinta idan yafuskanciwata matsala

فَالِابْنُ الَّذِي يَجِدُ فِي أُمِّهِ أُذُنًا تَسْمَعُ، وَقَلْبًا يَرْحَمُ، يَكُونُ أَكْثَرَ مَيْلًا إِلَى طَلَبِ النَّصِيحَةِ مِنْهَا، بَدَلًا مِنَ الْبَحْثِ عَنْهَا فِي مَصَادِرَ قَدْ تَضُرُّ بِدِينِهِ وَأَخْلَاقِهِ.

,Ɗan da yake samun uwa mai sauraro, da zuciya mai tausayi

,zai fi karkata wajen neman shawara daga gare ta

.maimakon ya nemi shawara daga wuraren da za su iya cutar da addininsa da ɗabi'unsa

وَالْحِوَارُ لَا يَعْنِي تَرْكَ الْحَزْمِ، كَمَا أَنَّ الْحَزْمَ لَا يَعْنِي الْقَسْوَةَ.

.Tattaunawa ba tana nufin barin tsayawa kan gaskiya ba

.Haka kuma tsayawa kan gaskiya ba yana nufin tsanani da rashintausayi ba

وَالتَّرْبِيَةُ النَّاجِحَةُ تَجْمَعُ بَيْنَ الْحُبِّ وَالرَّحْمَةِ وَالِانْضِبَاطِ.

.Tarbiyya mai nasara tana haɗa: ƙauna, da tausayi, da kumaladabtarwa

# ثَامِنًا: التَّعَاوُنُ بَيْنَ الزَّوْجَيْنِ أَسَاسُ الْأُسْرَةِ الصَّالِحَةِ

.Na takwas: Haɗin kai tsakanin ma'aurata shi ne tushen iyali nagari

لَا تَسْتَطِيعُ الْمَرْأَةُ وَحْدَهَا بِنَاءَ أُسْرَةٍ مُسْتَقِرَّةٍ إِذَا غَابَ التَّعَاوُنُ بَيْنَ الزَّوْجَيْنِ.

**Mace ita kaɗai ba za ta iya gina iyali mai kwanciyar hankali ba,idan**

**.babu haɗin kai tsakanin ma'aurata**

فَالزَّوْجَةُ تَحْتَاجُ إِلَى زَوْجٍ يُعِينُهَا، وَالزَّوْجُ يَحْتَاجُ إِلَى زَوْجَةٍ تُعِينُهُ.

**.Mata tana bukatar miji da zai taimaka mata**

وَالْأَبْنَاءُ يَحْتَاجُونَ إِلَى أَبٍ وَأُمٍّ يَعْمَلَانِ مَعًا مِنْ أَجْلِ مَصْلَحَتِهِمْ.

**Ya'ya kuma suna bukatar uba da uwa, waɗanda suke aiki tredomin'**

**.amfaninsu**

وَمِنَ الْمُعَاشَرَةِ بِالْمَعْرُوفِ أَنْ يَتَعَامَلَ الزَّوْجَانِ بِالِاحْتِرَامِ، وَأَنْ يَتَعَاوَنَا فِي تَرْبِيَةِ الْأَبْنَاءِ، وَأَنْ يَحْفَظَ كُلُّ وَاحِدٍ مِنْهُمَا أَسْرَارَ الْآخَرِ.

**,Daga cikin kyakkyawar zaman aure akwai**

**,ma'aurata su yi mu'amala da girmamawa**

**,su haɗa kai wajen tarbiyyar 'ya'ya**

**.kuma kowannensu ya kiyaye sirrin ɗayan**

وَأَلَّا يُحَوِّلَا الْخِلَافَاتِ الزَّوْجِيَّةَ إِلَى مَعَارِكَ أَمَامَ الْأَطْفَالِ.

**Kuma kada su mayar da sabanin da ke**

**.tsakaninsu zuwa rikice-rikice a gaban yara**

قَالَ اللهُ تَعَالَى:

**:Allah Maɗaukaki Ya ce**

﴿وَعَاشِرُوهُنَّ بِالْمَعْرُوفِ﴾

**"Kuma ku zauna da su cikin kyakkyawar mu'amala."**

فَالطِّفْلُ الَّذِي يَرَى أَبَاهُ وَأُمَّهُ يَتَعَامَلَانِ بِالرَّحْمَةِ وَالِاحْتِرَامِ يَتَعَلَّمُ أَنَّ الْأُسْرَةَ مَكَانٌ لِلْأَمَانِ.

**Yaron da yake ganin mahaifinsa da mahaifiyarsa suna mu'amalada rahama**

**,da girmamawa**

**.zai koyi cewa iyali wurin aminci ne**

بَيْنَمَا كَثْرَةُ الصُّرَاخِ وَالْإِهَانَةِ وَالْعُنْفِ تَتْرُكُ آثَارًا عَمِيقَةً فِي شَخْصِيَّتِهِ.

**,Amma yawan ihu, da zagi, da tashin hankali**

**suna iya barin mummunan tasiri mai zurfi a halayensa**

# تَاسِعًا: الْمَرْأَةُ الْمُسْلِمَةُ شَرِيكَةٌ فِي إِصْلَاحِ الْمُجْتَمَعِ

.Na tara: Mace Musulma abokiyar tarayya ce wajen gyaranal'umma

لَا يَنْتَهِي دَوْرُ الْمَرْأَةِ عِنْدَ حُدُودِ مَنْزِلِهَا؛ فَالْأُسْرَةُ الصَّالِحَةُ نَفْسُهَا لَبِنَةٌ فِي بِنَاءِ الْمُجْتَمَعِ الصَّالِحِ.

.Rawar mace ba ta ƙare a iyakar gidanta ba

.Domin iyali na gari da kansa tubali ne wajen gina al'umma ta gari

فَالْأُمُّ الَّتِي تُرَبِّي طَبِيبًا أَمِينًا، وَمُعَلِّمَةً مُخْلِصَةً، وَمُهَنْدِسًا نَافِعًا، وَتَاجِرًا صَادِقًا، وَدَاعِيَةً حَكِيمًا، وَمُوَاطِنًا صَالِحًا، تُشَارِكُ بِصُورَةٍ عَظِيمَةٍ فِي بِنَاءِ الْمُجْتَمَعِ.

Uwar da ta tarbiyantar da: likita mai aman da malamar da take daikhlasi,a, da injiniya mai amfani da ɗan kasuwa mai ,gaskiya

.da mai wa'azi mai hikima, da ɗan ƙasa na gari, tana ba da babbar gudummawa wajen gina al'umma

وَقَدْ قَالَ النَّبِيُّ ﷺ

:ya ce ﷺ Annabi

«مَنْ دَلَّ عَلَى خَيْرٍ فَلَهُ مِثْلُ أَجْرِ فَاعِلِه».

"Duk wanda ya shiryar zuwa ga wani alheri,

".yana da irin ladan wanda ya aikata shi

فَكُلُّ خَيْرٍ تَغْرِسُهُ الْمَرْأَةُ فِي أَبْنَائِهَا وَتُعِينُهُمْ عَلَيْهِ، يُمْكِنُ أَنْ يَمْتَدَّ أَثَرُهُ إِلَى الْآخَرِينَ.

Saboda haka, duk wani alheri da mace ta dasa a cikin 'ya'yanta,

kuma ta taimaka musu a kansa,

tasirinsa zai iya yaɗuwa zuwa ga wasu mutane.

وَلِهَذَا يَنْبَغِي لِلْمَرْأَةِ الْإِفْرِيقِيَّةِ الْمُسْلِمَةِ أَنْ تَنْظُرَ إِلَى رِسَالَتِهَا نَظْرَةً وَاسِعَةً.

Saboda haka ya kamata mace Musulma 'yar Afirka ta kallisakonta da

.hangen nesa mai faɗi

فَهِيَ لَا تَبْنِي بَيْتًا وَاحِدًا فَقَطْ، وَإِنَّمَا يُمْكِنُهَا أَنْ تُسْهِمَ فِي بِنَاءِ جِيلٍ كَامِلٍ.

.Ba gida ɗaya kawai take ginawa ba

.A'a, tana iya taimakawa wajen gina ƙarni gaba ɗaya

# عَاشِرًا: مُوَاجَهَةُ التَّحَدِّيَاتِ الْمُعَاصِرَةِ بِالْحِكْمَةِ وَالْإِيمَانِ

## .Na goma: Fskantar ƙalubalen zamani da hikima da imani

تُوَاجِهُ الْأُسْرَةُ الْمُسْلِمَةُ تَحَدِّيَاتٍ مُتَعَدِّدَةً، مِنْهَا الْفَقْرُ، وَالْبَطَالَةُ، وَالْخِلَافَاتُ الزَّوْجِيَّةُ، وَضَعْفُ التَّرْبِيَةِ الدِّينِيَّةِ، وَتَأْثِيرُ وَسَائِلِ الْإِعْلَامِ، وَتَسَرُّبُ بَعْضِ الْعَادَاتِ السَّيِّئَةِ إِلَى حَيَاةِ الْأَبْنَاءِ.

Iyali Musulmi suna fuskantar ƙalubale iri-iri. da rashin aikin yi,Daga cikinsu akwai talauci, da saɓanin ma'aurata, da raunintarbiyyar addini, da tasirin kafafen yaɗa labarai, da kuma .shigarwasu munanan ɗabi'u cikin rayuwar 'ya'ya

وَلَا يَكُونُ عِلَاجُ هَذِهِ الْمُشْكِلَاتِ بِالْيَأْسِ، وَإِنَّمَا بِالْعِلْمِ وَالْإِيمَانِ وَالتَّعَاوُنِ.

.Ba za a magance waɗannan matsaloli da yanke ƙauna ba

.A'a, ana magance su ne da ilimi, da imani, da kuma haɗin kai

فَعَلَى الْمَرْأَةِ أَنْ تَسْعَى إِلَى تَعَلُّمِ مَا تَحْتَاجُ إِلَيْهِ مِنْ أُمُورِ دِينِهَا.

Ya kamata mace ta yi ƙoƙarin koyon abubuwan .addininta da take buƙata

وَأَنْ تَسْتَفِيدَ مِنَ الْوَسَائِلِ التَّعْلِيمِيَّةِ النَّافِعَةِ.

.Kuma ta amfana da hanyoyin koyarwa masu amfani

وَأَنْ تَتَعَاوَنَ مَعَ زَوْجِهَا وَأَهْلِهَا وَالْمَدْرَسَةِ وَالْمُجْتَمَعِ فِي تَرْبِيَةِ الْأَبْنَاءِ.

,Kuma ta haɗa kai da mijinta, da iyalinta, da makaranta, da makaranta, da al'umma .wajen tarbiyyar 'ya'ya

كَمَا يَنْبَغِي أَلَّا تَخْجَلَ مِنْ طَلَبِ الْمَشُورَةِ مِنْ أَهْلِ الْعِلْمِ وَالْخِبْرَةِ، عِنْدَمَا تُوَاجِهُ مُشْكِلَةً لَا تَسْتَطِيعُ حَلَّهَا بِمُفْرَدِهَا.

,Haka kuma ai kamata ta ji kunyar neman shawara daga malamaida masu ƙwarewa ba .idan ta fuskanci matsalar da ba za ta iya magance ta ita kaɗai ba

# الْحَادِيَ عَشَرَ: أَجْرُ تَرْبِيَةِ الْأَبْنَاءِ فِي الْإِسْلَامِ

.Na goma sha ɗaya: Ladan tarbiyyar 'ya'ya a Musulunci

أَيَّتُهَا الْأُمُّ الْمُسْلِمَةُ، إِنَّ تَرْبِيَةَ الْأَبْنَاءِ لَيْسَتْ مَسْؤُولِيَّةً دُنْيَوِيَّةً فَقَطْ، بَلْ هِيَ مِنْ أَبْوَابِ الْأَجْرِ وَالْقُرْبِ مِنَ اللهِ تَعَالَى.

.tarbiyyar 'ya'ya ba nauyin duniyakawai ba ne

.Ya ke uwa Musulma, A'a, tana daga cikin kofofin samun lada da kusanci da Allah Maɗaukaki

إِذَا أَخْلَصْتِ النِّيَّةَ لِلَّهِ، وَصَبَرْتِ عَلَى مَشَقَّةِ التَّرْبِيَةِ، وَقَصَدْتِ بِهَا إِعْدَادَ أَبْنَاءٍ صَالِحِينَ يَعْبُدُونَ اللهَ وَيَنْفَعُونَ النَّاسَ.

,Idan kika tsarkake niyyarki domin Allah, kuma kika yi hakuri da wahalar tarbiyya

,kuma kika yi niyyar shirya 'ya'ya nagari waɗanda za su bauta wa Allah

.kuma su amfanar da mutane

قَالَ رَسُولُ اللهِ ﷺ:

:ya ce ﷺ Manzon Allah

ِذَا مَاتَ الْإِنْسَانُ انْقَطَعَ عَمَلُهُ إِلَّا مِنْ ثَلَاثَةٍ: صَدَقَةٍ جَارِيَةٍ، أَوْ عِلْمٍ يُنْتَفَعُ بِهِ، أَوْ وَلَدٍ صَالِحٍ يَدْعُو لَهُ

"Idan mutum ya mutu, aikinsa yana yankewa, sai dai abubuwauku:

".sadaka mai gudana, ko ilimin da ake amfana da shi, ko ɗa nagari da yake yi masa addu'a

وَهَذَا الْحَدِيثُ يُبَيِّنُ عِظَمَ نِعْمَةِ الْوَلَدِ الصَّالِحِ.

Wannan hadisi yana bayyana girman ni'imar samun ɗa na gari.

فَصَلَاحُ الِابْنِ لَا يَنْفَعُهُ وَحْدَهُ، بَلْ يُمْكِنُ أَنْ يَمْتَدَّ أَثَرُهُ إِلَى وَالِدَيْهِ بَعْدَ وَفَاتِهِمَا مِنْ خِلَالِ دُعَائِهِ لَهُمَا وَأَعْمَالِهِ الصَّالِحَةِ.

.Domin nagartar ɗa ba shi kaɗai take amfanarwa ba

,A'a, tasirinta zai iya kaiwa ga iyayensa bayan mutuwarsu

.ta hanyar addu'arsa gare su, da ayyukansa na gari

فَكَمْ مِنْ أُمٍّ سَهِرَتْ عَلَى تَرْبِيَةِ وَلَدِهَا، وَعَلَّمَتْهُ الْقُرْآنَ، وَأَمَرَتْهُ بِالصَّلَاةِ، وَرَبَّتْهُ عَلَى الصِّدْقِ وَالْأَمَانَةِ، وَصَبَرَتْ عَلَى أَخْطَائِهِ.

,Babu kididdigar yawan iyaye mata da suka yi dare suna kula da tarbiyyar 'ya'yansu

,suka koya musu Alkur'ani, suka umarce su da sallah

,suka tarbiyantar da su a kan gaskiya da amana

.kuma suka yi hakuri da kurakuransu

# الثَّانِيَ عَشَرَ: نَمَاذِجُ مِنَ الصَّحَابِيَّاتِ فِي تَرْبِيَةِ الْأَجْيَال

Na goma sha biyu: Misalai daga cikin sahabbai mata
.wajentarbiyyar tsararraki

ثُمَّ أَصْبَحَ شَابًّا صَالِحًا يَنْفَعُ النَّاسَ.

.Daga baya sai ya zama matashi na gari mai amfanar mutane

إِنَّ تَعَبَهَا لَمْ يَذْهَبْ سُدًى، بَلْ هُوَ بِإِذْنِ اللهِ مِنَ الْأَعْمَالِ الَّتِي يُرْجَى لَهَا الْأَجْرُ الْعَظِيمُ.

.Lallai wahalar da ta sha ba ta tafi a banza ba
,A'a, da izinin Allah
.tana daga cikin ayyukan da ake fatan samun babban lada a kansu

وَقَدْ قَالَ النَّبِيُّ ﷺ:

:ya ce ﷺ Annabi

«مَنْ دَلَّ عَلَى خَيْرٍ فَلَهُ مِثْلُ أَجْرِ فَاعِلِهِ».

"Duk wanda ya shiryar zuwa ga wani alheri,
".yana da irin ladan wanda ya aikata shi

فَالْأُمُّ الَّتِي تُعَلِّمُ ابْنَتَهَا الصَّلَاةَ، أَوْ تُعَلِّمُ ابْنَهَا قِرَاءَةَ الْقُرْآنِ، أَوْ تَغْرِسُ فِي قَلْبِهِ الصِّدْقَ، أَوْ تَدُلُّهُ عَلَى بِرِّ الْوَالِدَيْنِ، أَوْ تُحَذِّرُهُ مِنَ الظُّلْمِ وَالْحَرَامِ، هِيَ فِي الْحَقِيقَةِ تَدُلُّهُ عَلَى الْخَيْرِ، وَتَرْجُو مِنَ اللهِ أَجْرًا عَلَى ذَلِكَ.

Uwar da take koya wa 'yarta sallah,
ko ta koya wa ɗanta karatun Alkur'ani,
ko ta dasa gaskiya a cikin zuciyarsa,
ko ta shiryar da shi zuwa ga biyayyar iyaye,
ko ta grgaɗe shi daga zalunci da haram,
a gaskiya tana shiryar da shi zuwa ga alheri.
Kuma tana fatan samun lada daga Allah saboda hakan.

التَّرْبِيَةُ عِبَادَةٌ تَحْتَاجُ إِلَى نِيَّةٍ صَالِحَةٍ

.Tarbiyya ibada ce da take buƙatar kyakkyawar niyya

قَدْ تَقُومُ الْمَرْأَةُ بِالْأَعْمَالِ نَفْسِهَا الَّتِي تَقُومُ بِهَا غَيْرُهَا، وَلَكِنْ تَخْتَلِفُ الْأُجُورُ بِاخْتِلَافِ النِّيَّاتِ.

,Mace za ta iya yin ayyukan da wata mace take yi
.amma lada yana bambanta gwargwadon niyya

فَإِذَا قَالَتِ الْأُمُّ فِي نَفْسِهَا: «أَنَا أُرَبِّي أَبْنَائِي ابْتِغَاءَ مَرْضَاةِ اللهِ، وَأُرِيدُ أَنْ يَكُونُوا عِبَادًا صَالِحِينَ، وَأَنْ يَنْفَعُوا الْإِسْلَامَ وَالْمُسْلِمِين

:Idan uwa ta yi niyya a zuciyarta ta ce
Ni ina tarbiyantar da 'ya'yana ne domin neman yardar Allah.Ina son su kasance bayi nagari. Kuma ina son su amfanar da"
".Musulunci da Musulmai

تَحَوَّلَتْ أَعْمَالُهَا الْيَوْمِيَّةُ إِلَى عِبَادَةٍ يُرْجَى لَهَا الْأَجْرُ.

,To ayyukan da take yi kullum za su koma ibada

.wadda ake fatan samun lada a kanta

